# Takaitaccen bayani

## Matsayar Duniya a kan
## Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i

Wannan taƙaitaccen bayani na bawa ƙungiyoyi masu zaman kansu (wato CSOs) bayani da aka taƙaita a kan ka'idoji da shawarwari na ƙasa da ƙasa a kan ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i (SEAH). Yana da mahimmanci ga ƙungiyoyi masu zaman kansu wato CSOs su cika ka'idodin da suka dace lokacin da suke ba da ayyukan cigaba da ayyukan jin ƙai domin kare ma'aikata kuma ka da a yi illa a cikin al'ummomin da kuke aiki.

**Matsayar duniya da kayan aiki na magance Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH**

A cikin shekarun 2018 da 2019 manyan masu ba da gudummawa na gwamnati waɗanda suka kafa Kwamitin Taimakon da Ci Gaba (DAC) na Kungiyar Haɗin Gwiwar Tattalin Arziki da Ci Gaba wato OECD sun yi yarjejeniya a kan aikinsu da na duk abokan aikinsu su bi ka'idojin Kwamitin tattaunawa na Kungiyoyin Agaji wato IASC da/ko Matsayar Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji wato CHS (1-3 da ke kasa). Dafrtarin Kiyaye Lafiyar Yara wato KCS (4 da ke ƙasa) ya fi dacewa ga ƙungiyoyi masu aiki tare da yara. Shawarar Kwamitin Taimakon da Ci Gaba wato DAC ta shekarar 2019 (5 a ƙasa) kayan aiki ne na ƙasa da ƙasa da aka yi nufi don gwamnatocin masu ba da gudummawa, amma an haɗa su anan don ƙungiyoyi su fahimci abin da masu ba da kuɗi suka himmatu a kai da kuma hanyoyin haɗi ga ka'idodin Kwamitin tattaunawa na Kungiyoyin Agaji wato IASC da Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji wato CHS waɗanda za su fi dacewa kai tsaye.

### 1 Manyan Ka'idoji Shida na Kwamitin tattaunawa na Kungiyoyin Agaji Da Suka Shafi Ci da gumi da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i

**Me ya sa Matsayar ta wanzu?** A sakamakon zarge-zargen SEAH da aka yi na yammacin Afirka a shekara ta 2002 Kwamitin tattaunawa na Kungiyoyin Agaji (IASC) ta kafa Runduna ta Musamman kan Kariya daga Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i (PSEA) a cikin rikice-rikicen jin kai. An wajabtawa rundunar su karfafa kariya da kula da mata da yara musamman a yanayi na rikicin bil adama da sabani, musamman bayar da shawarwari masu nufin kawar da Ci da gumi da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i(SEA). Wani muhimmin abu da ya fito shi ne ainihin ƙa'idoji guda shida waɗanda ke samar da ka'idojin aiki a kan mafi ƙarancin ɗabi'ar da aka amince da ita wanda aka aiwatar a cikin gajeriyar sanarwar Babban Sakatare na Majalisar Dinkin Duniya (ST/SGB/2003/13).

**Menene wannan Matsaya ta ƙunsa?** Matsayar: yana buƙatar a ɗauki Ci da gumi da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i wato SEA a zaman babban rashin da'a, da yiwuwar kora daga aiki; yana kuma hana ma'aikata biyan kuɗi domin jima'i ko musayar kaya da dai sauransu don jima'i; da kuma haramta yin jima'i da duk wanda bai kai shekara 18 ba; da kuma hana alaƙa mai ci da gumi tare da masu cin

gajiya da ko abokan tarayya; da wajabtawa ma'aikata su bayar da rahoton damuwa; da kuma wajabtawa ma'aikata ƙirƙirar al'ada wadda ke hana Ci da gumi da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i wato SEA.

**Wa Matsayar ta shafa?** Duk ma'aikatan Majalisar Dinkin Duniya (UN) da duk wanda ke aiki tare da/karbar kudade daga gare su. Idan kuna da haɗin gwiwa da Majalisar Dinkin Duniya (ko wasu ƙungiyoyi waɗanda ke bin waɗannan ƙa'idojin, misali Cibiyoyin Kuɗi na Duniya (IFI)), dole ne ku yarda ku bi waɗannan ƙa'idodin domin hana Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i wato SEA.

## 2 Mafi ƙarancin Matsayar Aiwatarwa na Kwamitin tattaunawa na Kungiyoyin Agaji: Kariya daga Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i da Ma'aikatan Cikin Gida (MOS-PSEA)[1]

**Meye ya sa aka ajiye wannan Matsayar?** Da farko an tsara shi ne domin daidaita yadda Majalisar Dinkin Duniya wato UN da duk wanda ke samun tallafin Majalisar Dinkin Duniya wato UN kare membobin al'umma daga fuskantar amfani da dama ta hanyar jima'i da cin zarafi daga ma'aikatansu. Bai hada da tursasawa ta hanyar jima'i na ma'aikata a wurin aiki. Sauran kungiyoyi, musamman wasu manyan cibiyoyin hada-hadar kudi na ƙasa da ƙasa, su ma suna amfani da ita. International Council of Voluntary Agencies (ICVA), InterAction da Steering Committee don Humanitarian Response (SCHR) duk masu gayyata ne na dindindin zuwa Kwamitin tattaunawa na Kungiyoyin Agaji wato IASC.

**Me wannan Matsaya ta ƙunsa?** Wannan Matsayar na buƙatar ƙungiyar da abokan haɗin gwiwarta su kasance suna da manufa da ke ajiye domin hana Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i wato SEA. Ma'aikatan gida da abokan aiki dole ne su sanar da al'ummomin yankin game da matakan da ofishinsu na gida da abokan aiki ke ɗauka domin hana Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i wato SEA. Waɗannan matakan sun haɗa da samar da tsarin da ya dace da al'ada domin kowa ya bayar da rahoton damuwa da samun tallafi, ciki har da mambobin al'umma da ma'aikata, tabbatar da tsarin ɗaukar aiki ya gano mutanen da suka dace a ɗauka haya, da horar da ma'aikata yadda za su aiwatar da Matsayar.

Matakin na buƙatar ƙungiyoyi su samu keɓaɓɓen wuri ko masu jagora na Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i wato SEA, bayyanannun ƙa'idojin aiki da tabbatar da cewa an sanya Gajeruwar Sanarwar Babban Sakatare (ST/SGB/2003/13) ko ka'idojin aiki daban-daban cikin kwantiragi.

**Wa Matsayar ta shafa?** Duk ma'aikatan Majalisar Dinkin Duniya da duk wanda ke aiki da ko karbar kudade daga wurinsu. Idan kun haɗa gwiwa da Majalisar Dinkin Duniya, dole ne ku yarda ku bi waɗannan ƙa'idojin domin hana ci da gumi da cin zarafi ta hanyar Jima'i. Masu ba da gudummawa na Kwamitin Agaji da Cigaba wato DAC na buƙatar bin Kariya daga Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i da Ma'aikatan Cikin Gida wato MOS-PSEA da/ko Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji wato CHS. Duk dAftarin guda uku sun tsara tushen manufofin Shawarar Kwamitin Agaji da Cigaba wato DAC (duba aya ta 5 a ƙasa).

## 3 Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji a kan Inganci da Ɗaukar Alhaki (CHS)[2]

1 https://interagencystandingcommittee.org/system/files/3_minimum_operating_standards_mos-psea.pdf
2 https://corehumanitarianstandard.org/the-standard

**Meye yasa aka ajiye wannan Matsayar?** Wannan Matsaya tana samar da hanyar yau da kullum wajen isar da taimakon jin kai ga al'ummomin da rikici ya shafa. Wannan kuma ya haɗa da yadda ake hana da mai da martani kan Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH, mai ɗauke da buƙatu iri ɗaya ga Kariya daga Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i da Ma'aikatan Cikin Gida wato MOS PSEA. Yawan duƙufa a akan Matsaya ta Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji, idan an cika su, su ma suna bayar da gudummawa ga ƙirƙirar ƙungiyoyi masu aminci.

**Menene wannan Matsaya ta ƙunsa?** Wannan Matsayan na buƙatar gano da magance haɗarorin Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH da ke cikin ƙungiyoyi da ayyukan shirye-shiryensu. Dole ne ƙungiyoyi su kasance suna da manufofi na hanawa da mayar da martani ga Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH. Dole ne a sanar da al'umma game da aikin kungiyar wajen hana Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH. Dole ne tsarin bayar da rahoto ya kasance domin al'ummomi su bayar da rahoto. Bayar da rahotanni da hanyoyin bincike dole ne su ba da fifiko kan aminci, buƙatu da tunanin waɗanda abu ya shafa da waɗanda suka tsira. An [buga fihirisar Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji CHS Kariya daga Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato PSEAH a cikin 2020](), lokacin da aka saka barazana da nufin jima'i a karo na farko.

**Wa Matsayar ta shafa?** An rubuta Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji wato CHSdomin aikin jin kai amma Kungiya na Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji wato CHS Alliance ta ba da shawarar cewa duk wanda ke bayar da ayyukan cigaba zai iya amfani da ita.

## 4 Tsayayyun Ka'idojin Kare Yaro/Yarinya na Duniya wajen Kiyaye Lafiyar Yara[3]

**Me ya sa aka samar da wannan Matsayar?** Domin kare yara daga duk wani nau'i na tashin hankali da cin zarafi, ciki har da Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i wato SEA, wanda zai iya tasowa ga yara daga taimakon jin kai ko cigaba da ake bayarwa.

**Menene wannan Matsaya ta ƙunsa?** Wannan Matsaya na buƙatar duka ƙungiyoyin da ke hulɗa da yara ya zama suna da ka'idar kare yara a tanade. Matsayar na tabbatar da duk wanda ke aiki tare da yara an horar da shi ko ita kuma an tallafa masa wajen kare yara. Dole ne ƙungiyoyi su haɗa matakan kiyaye yara a dukan ayyuka da tsare-tsare na ƙungiya. Dole ne tsarin bayar da rahoto ya kasance akwai shi ga duk wanda ke son bayar da rahoto na wata damuwa, musamman yara.

**Wa Matsayar ta shafa?** Waɗannan ƙa'idojin na sa kai ne ga kowace ƙungiya amma sun fi dacewa da ƙungiyoyi waɗanda aikinsu ya ƙunshi, ko tasirinsu yake ga, yara.

## 5 Shawarwari Na Kwamitin Taimakon Da Ci Gaba Na 2019[4] A Kan Kawo KarshenCi da gumi, Cin Zarafi Da Tursasawa A Cikin Haɗin Kai Na Ci Gaba Da Taimakon Jin Kai[5]

3 https://www.keepingchildrensafe.global/wp-content/uploads/2020/02/KCS-CS-Standards-ENG-200218.pdf

4 Kungiyar Haɗin Gwiwar Tattalin Arziki da Ci Gaba (OECD) kungiya ce ta ƙasa da ƙasa da ke aiki tare da gwamnatoci, masu tsara manufofi da yan kasa domin bunkasa manufofi da ka'idojin ƙasa da ƙasa wadanda ke inganta daidaito da dama ga kowa. Kungiyar Haɗin Gwiwar Tattalin Arziki da Ci Gaba wato OECD tana da Kwamitin Taimakon da Ci Gaban (DAC) wanda ya haɗa wasu manyan masu bayar da taimakon na cigaba a duniya wuri guda domin sa ido kan yadda ake amfani da kudade, samar da matsaya da kuma lura da ayyukan mambobi a kan taimakon ci gaba. A halin yanzu akwai mambobin Kwamitin Taimakon Da Ci Gaba wato DAC guda 30. https://www.oecd.org/dac/development-assistance-committee/

5 http://www.oecd.org/officialdocuments/publicdisplaydocumentpdf/?cote=DCD/DAC(2019)31/FINAL&docLanguage=En

**Me yasa daftarin ya wanzu?** Gwamnatocin da ke bayar da kudade domin ayyukan cigaba da ayyukan jin kai sun so daidaita aikinsu domin hana da mayar da martani ga Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH.

**Me daftarin ya shafa?** Yana ba da fifikon haƙƙoƙi, buƙatu da buƙatun waɗanda suka tsira da waɗanda ke fama da Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH. Kungiyoyin da suka karɓi kuɗi dole ya kasance suna da manufofi da ka'idojin aiki da ke kula da Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH. Dole ne tsarin bayar da rahoto na boye suna da na sirri ya kasance akwai shi ga duk wanda ke son ba da rahoto. Wannan ya haɗa da mambobin ma'aikata da mambobin al'umma. Ya kamata ƙungiyoyi su adana bayanan matakan kiyayewa da suke aiwatarwa. Wannan yana ba su damar yin la'akari da nasarorin da suka samu da kuma tunanin abin da za su inganta.

Hadin takardan da kanta ta amince da *"Ka'idodin Tsayayyen Kwamitin Tsakanin Hukumomi da Mafi Karancin Ka'idodin a kan Rigakafin Ci da gumi da Cin Zarafi ta hanyar Jima'i (MOS-PSEA), tare da Muhimman Ka'idodin Aikin Agaji a kan Inganci da Ɗaukan Alhaki (CHS), a matakin mahimmiyar Matsaya na ƙasa da ƙasa".* Don haka, Shawarar Kwamitin Taimakon da Ci Gaba wato DAC ba ta ƙirƙiri sabuwar matsaya ba, amma tana mayar da hankali kan aikace-aikacen masu ba da gudummawa a kan amfani da ƙa'idojin Kwamitin tattaunawa na Kungiyoyin Agaji wato IASC da Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji wato CHS.

**Su wanene za su yi aiki da daftarin?** Gwamnatoci da suke mambobi na Kwamitin Taimakawa Cigaba da duk wata kungiya da ke aiki da su a tabbatar cewa shi ke jagorantar aikinsu na Ci da gumi da Cin Zarafi da Barazana ta Hanyar Jima'i wato SEAH. Ana kuma ƙarfafa gwiwar gwamnatoci da ƙungiyoyin da ba mambobin Kwamitin Taimakon da Ci Gaban ba su 'bi' daftarin kuma ƙungiyoyin Majalisar Dinkin Duniya da yawa sun yi hakan.

Don amfani da ƙa'idojin da kayan aikin ƙasa da ƙasa da aka jera a sama, sai a koma zuwa ga RSH How-to Note on applying SEAH sector standards.